# Domin Yara
# ADDU'AR ALKAWALI

**ALHERI** Ya uba na cikin sama na gode da ka kaunace ni, ka kuma maishe ni daya daga cikin 'ya'yanka.

**KAUNA** Ka taimakeni in kaunace ka in kuma yi maka biyayya.

**TAUSAYI** Ka taimake ni in kaunaci wadansu kamar yadda ka kaunace ni.

**TUBA** Ina bakin ciki domin zunubai na. Ka wankeni sarai.

**SUJADA** Zan yabe ka da dukan zuciya ta!

**MIKA KAI** Yesu, ina son in bika, ka zama Ubangiji na. Ka maishe ni yadda ka ke so.

**DOGARA** Ka cika ni da Ruhun ka Mai Tsarki.

**TASIRI** Ka maishe ni kayan aikin na na alheri, gaskiya da adalci.

**ALMAJIRANCI** Ka yi amfani dani domin daukakarka, in kuma gayyaci wadansu su bika.

**IKO DA DOKA** A cikin sunan Yesu na yi addu'a. Amin.

**BIN YESU TARE**

thepraye rcovenant.org/kids

# AYOYIN HADACEWA

**Missalin battaciyar tunkiya · Luka 15:1-17** | Ku dubi irin kaunar da Uba ya nuna mana, har yake ce da mu 'ya'yan Allah, haka kuwa muke. –1 Yahaya 3:1

**Labarin Ibrahim · Farawa 12:1-5** | Ya ce masa, "Ka kaunaci Ubangiji Allahnka da dukkan zuciyarka, da dukkan ranka, da dukkan hankalinka. Wannan shi ne babban umarni na farko. –Matiyu 22:37-38

**Basamariye da ya nuna jinkai · Luka 10:25-37** | Wannan fa shi ne umarnina, cewa, ku kaunaci juna kamar yadda na kaunace ku. –Yahaya 15:12

**Misalin bawa wanda bai yafe ba · Matiyu 18:21-35** | Ka wanke muguntata sarai, Ka tsarkake ni daga zunubina! –Zabura 51:2

**Labarin Kirisimati · Luka 2:1-20** | Zan yabe ka da zuciya daya, ya Ubangiji, Zan hurta dukan abubuwa masu banmamaki da ka yi. –Zabura 9:1

**Bitrus ba cikakke ba ne · Luka 22:52-62** | Kuna kirana Malam, da kuma Ubangiji. Daidai ne kuwa, don haka nake. –Yahaya 13:13

**Mai taimako · Yahaya 14:15** | Sai dai ku cika da Ruhu… –Afisawa 5:18b

**Yesu da kananan Yara · Matiyu 18:1-6** | Kalman nan kuwa ya zama mutum, ya zauna a cikinmu, yana mai matukar alheri da gaskiya. Mun kuma dubi daukakarsa, daukaka ce ta makabaicin Da daga wurin Ubansa. –Yahaya 1:14

**Shawulu ya zama Bulus · Ayukan Manzani 9:1-22** | Don haka sai ku je ku almajirtar da dukkan al'ummai, kuna yi musu baftisma da sunan Uba, da Da, da Ruhu Mai Tsarki. –Matiyu 28:19

**Bartimayus makaho · Matiyu 10:46** | Saboda haka ne kuma Allah ya daukaka shi mafificiyar daukaka, ya kuma yi masa baiwa da sunan nan da yake birbishin kowane suna. –Filibiyawa 2:9

40 DAY PRAYER COVENANT For Kids!
4/14 window movement
FIND US ON YouVersion
(+228) 90 19 36 46
©2014 The 40 Day Prayer Covenant Inc. All rights reserved